**KOMAI NISAN JIFA**

**EPISODE 19**

**Characters**

*Danjuma*

*Tina*

*Hannah*

*Laraba*

*Kande*

*Dr. Daoud*

*Alh. Bature*

**SCENE 1**

*NORTHERN KADUNA, HEALTH CENTRE MORNING*

| | |
|---|---|
| **1. MUSIC:** | **THEME MUSIC** |
| 2. **SFX:** | **OFF MIC HURRYING STEPS, SOUNDS OF PATIENTS TALKING OUTSIDE, DOOR OPENS AND CLOSES.** |
| 3**. DR. DAOUD:** | Alhaji Bature, ina kwana, shiga mana ka zauna me ya faru? |
| 4**. ALH. BATURE**: | Na gode likita, sakamakon gwajina na haihuwa ya fito? |
| 5. **DR. DAOUD:** | Sakamakon ya fito. |
| 6. **ALH. BATURE:** | **(EAGERLY)** me sakamakon ya nuna? |
| 7. **DR. DAOUD:** | Sakamakon gwajin ya nuna cewa kana da karancin maniyi. |
| 8. **ALH. BATURE:** | **(TAKEN ABACK**) Mene? Me ka ke nufi? Don Allah likita gaya mun manufar shi. (INCENSED) ina fatan ka san ina da yara uku mata. |

9. **DR. DAOUD:** **(PATIENTLY)** Duk da haka, abin da yake nufi shine maniyin ka bashi da karfi sosai da zai iya kyankyashe kwan abokiyar zaman ka har ta dauki ciki.

10. **ALH. BATURE**: Mhn. Haka ne?

11. **DR. DAOUD**: Haka ne, amma duk da haka mutane da yawa masu karancin maniyi sun haifi yara da yawa kamar yadda kayi.

12. **ALH. BATURE:** **(ANGRILY)** Amma likita har yanzu na kasa gane inda wanan abu zai same ni. Ka san ko ni waye a cikin wannan alummar?

13. **DR. DAOUD:** Alhaji kayi hakuri, amma abin da sakamakon ya nuna kenan, watakila dalilin daya sa matarka ta kasa samun ciki kenan. Don Allah ka kwantar da hankalinka.

14. **ALH. BATURE:** **(TALKING ANGRILY)** yaya zaka ce inyi hakuri? Ban yarda b azan iya haihuwa ba Ni namiji ne.

15. **DR. DAOUD:** **(GENTLY EXPLAINING)** Don Alhaji ka yi hakuri, karancin maniyi bay a nufin mutum ba zai haihu ba, abin da yake damun ka shi muke kira infertility kuma akwai abin da za ayi maka da zai magance wannan matsalar.

16. **ALH. BATURE**: Idan duk abin da kake cewa gaskiya ne, a ina za'a yi min wannan magani?

17. **DR. DAOUD:** Kana wurin daya dace. Asibitin tazarar haihuwa ya na bada shawarwari har ma ga wanda suke kokarin haihuwa.

18. **ALH. BATURE**: Toh idan haka ne, me kaga ya dace da inyi?

19. **DR. DAOUD:** Ina jin ya kamata ku zo da matarka wurin bayar da maganin tare saboda ku shawarta me ya dace da kuyi.

20. **ALH. BATURE**: Kan dan bani lokaci inyi tunani

21.**DR. DAOUD**: Babu damuwa Alhaji, amma bana son ka tayar da hankalinka. Ka zo wurin daya dace, za kuma mu taimaka maka. Babu damuwa, ka gane?

22. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**SCENE 2**

*SOUTHERN KADUNA: DANJUMA AND HANNAH'S COMPOUND*

23**. SFX:** **<u>SOUND OF DOOR OPENING (ON MIC) SOUND OF PLATES AND POTS CLINKING TOGETHER, DANJUMA COMES INTO THE KITCHEN.</u>**

24. **DANJUMA:** Ina wuni tina… Matana bata dawo bane?

25. **HANNAH:** Ta dawo a takaice, ta shiga uwar daki, kuma ta koma ba tare dagaya mun inda zata jeba.

26. **DANJUMA:** **(CONCERNED)** Nayi mamaki da bata tayar dani daga barci ba kuma yadda ban tashi ba lokacin da ta shiga dakin.

27. **TINA:** Yaya Danjuma, kamar kana yin aiki da yawa. Baka cinye abincinka ma. Kamar ma yanzu ka tashi barci, ka shiga dakin ka kuma barci ya kwashe ka.

28. **DANJUMA:** Haka ne, bana jin dai dai tunda na ci abincin nan bazan iya tuna lokacin da na shiga daki bama kuma jikina na ciwo musamman ma kai na.

29. **TINA:** **(CONCERNED**) Eyyah. Ko in samo maka maganin zazzabi ko zaka sha perpesun kifin nan da nakeyi.

30. **DANJUMA:** **(DISTRACTED**) A, a yanzu ba lokacin ba ne, Tina Bari in nema Hannah a waya.

31. **SFX:** <u>**SOUND OF PHONE NUMBER BEING ENTERED ON A PHONE**</u>.

32. **DANJUMA:** Bata amsa wayarta, Tina.

33. **TINA:** Ina jin bata kusa da wayar ne. Na tabbata zata kira ka idan tag a lamabar ka.

34. **DANJUMA:** Amma wannan ba dabiyar Hannah bace. Kin tabbata bata baki sako ki gaya mun ba.

35. **TINA:** Ko da yake Danjuma, ka yi la'akari da canjin yanayin nan na Hannah ya farune saboda cikin da ta ke dauke dashi. Ka san tana nuna wnai hali na daban.

36. **DANJUMA:** Kai, Tina bana jin wannan ne matsalar. Ina jin wannan ba dalili bane.

37. **TINA:** Idan bah aka bane, me yasa bata daukar wayanta, Danjuma?

38. **DANJUMA:** Ina jin wani abu ya fasu tanda har yanzu Hannah bat a dawo ba… Ina hin ya kamata inje in dubuata. Watakila wani abu ya faru d aita kuma tana bukatar taimako na.

39. **TINA:** **(IRRITATED)** Danjuma, ka na jin akwai bukatar haka? Baka san ko ina taje ba. Don Allah ka kwantar da hankalinka, kaci abinci. Abinci ya nuna.

40. **DANJUMA:** **(UPSET)** Kalli Tina, yanzu ba lokacin abinci ba ne. ya kamata in tafi in nemo matata. Ina dai fatan tana lafiya.

41. **MUSIC:** <u>**BRIDGE MUSIC**</u>

**SCENE 3**

*NORTHERN KADUNA: HAJIYA INNA'S HOUSE*

42. **SFX:** **<u>(SOUND OF FOOTSTEPS DOOR OPENS AND CLOSES HANNAH COMES IN TEARFULLY)</u>**

43. **LARABA:** Hannah! Haba me ki ke yi anan? Me ya faru? Me ya sa kike Kuka?

44. **HANNAH:** **(SOBBING)** L-I-I Laraba… Ina fata baki da mu ba. Hajiya inn ace ta ganni a waje tace wai in zo dakin ki. (WAILS).

45. **LARABA:** **(PLEADINGLY)** Ba damuwa. Don Allah Hannah ki daina kuka, ka gaya mun abin day a faru

46. **HANNAH:** **(SOBBING)** Tina ce...

47. **LARABA:** Me yafaru da ita?

48. **HANNAH:** Ba kome (STILL SOBBING) na ganta ta Fito dag a uwar dakin mu bayan nazo kusa da ita, sai naga Danjuma yana barci a cikin uwar dakin.

49. **LARABA:** **(SHOCKED)** Hannah! Ba'a ki keyi. Kin tabbata ba karya Tina ta keyi ba?

50. **HANNAH:** **(BITTERLY)** Kalli Laraba, zan rantse da duk wani abu da na sani cewa ba gaskiya ba ne, ba dan na gani da Idanuna ba.

51. **LARABA:** Kai/kalli wahala! Toh me Danjuma y ace don kare kanshi.

52. **HANNAH:** **(TEARFULLY)** Yaki tashi ya gaya mun amma Tina ta gayamun cewa sun dade suna wannan dangantakan a asirce.

53. **LARABA:** **(SHOCKED)** Idan dai hakane, Danjuma ya bani kunya. Amma ina zuwa, Hannah, wane irin barci ne Danjuma yakeyi har ya kasa tashi duk da wannan rikici da ke faruwa.

54. **HANNAH:** Ban sani bafa Laraba, amma a gaskiya na rasa yadda zan yarda da abin da nagani.

55. **LARABA:** Don Allah Hannah ki kwantar da hankalinki, ina jindai wni abu wafaru. Akwai bukatar bayani anan.

56. **HANNAH:** **(SOBBING GENTLY)** A gaskiya ban san abin da zanyi ba laifi ne dana jawo Tina ta zauna da ni? Haka za ta biya ni?

57. **LARABA:** Kada ki takurawa kanki

58. **HANNAH:** Zan iya jure da cin amanar da Tina ta yi mun. Dama yaruwace ta nesa, ba saninta nayi sosai ba. Amma ban taba tunanin Danjuma zaici amanita kamar haka ba. (**BURST INTO TEARS AGAIN)**.

59. **LARABA:** Ya Isa Hannah. Ina jin ya kamara muje muyi Magana da mahaifiyarki kande, watakila zata taimaka a shawo kan matsalar.

60. **HANNAH:** **(CALMS DOWN A LITTLE)** Na gode da kika zama kawa ta gari. Kiyi hakuri na dame kid a matsalolina ban ko tambayeki yaya kike ba.

61**. LARABA**: Don Allah karki damu dani saboda halinda kike ciki a yanzu yafi mahimmanci.

62. **HANNAH:** Kawata kada ki damu, zan so abin da zai dauke mun hankilina domin in manta da wannan bakin cikin. Don Allah gaya mun me yake faruwa dake.

63. **LARABA:** Mun bata da Dr. Daoud. Ya gaya mun tarihinsa, yadda ya rasa iyalinsa gaba daya ta hanyar da ban gamsu da tarihin ba idan na kwatantashi da mummunar tarihin shi yasa nag a ba mu dace da juna ba.

64. **HANNAH:** Ban yarda cewa zaman ku tare mumunar Isharabace. Kinga abu mara kyau yak an faru da mutane masu halin kwarai-akowane lokaci.

65. **LARABA:** Amma lamarin mu daban ne! Ina ganin rabuwar mu yafi fa'ida.

66. **HANNAH:** Haba Kawata ki daina fadin haka, na tabbata abin daya faru da ku ba wai tsinuwa bace ko wani abu. Don Allah laraba ki baiwa Dr. Daoud dama.

67. **LARABA**: Hannah kin tabbata? Ina jiye mana tsoro.

68. **HANNAH**: Ya kamata kiyi karfin hali ki baiwa Dr. Daoud wata dammar.

69.**LARABA:** Naji Hannah, kada mu damu da matsalolina mu maid a hanakali a kanki, ko? Zo mu tafi wuri mahaifiyar ki.

**70. MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**SCENE 4**

*NORTHERN KADUNA: KANDE HOUSE IN THE EVENING*

71. **SFX:** **SOUND OF FRANTIC KNOCKING IN THE DOOR**

72. **KANDE:** Waye ne?

73**. SFX:** **DOOR OPENS**.

74. **KANDE:** **(COLDLY)** Na tabbata kai ne.

75. **DANJUMA:** **(PANICKY GREETINGS)** Barka da rana Gwaggo Kande. Nazo kan maganar Hannah ne.

76. **KANDE:** **(COLDLY)** Na tabbata kai ne…

77. **DANJUMA:** **(CONFUSED)** Erm hakane amma ko da yake, Gwaggo kande, ina nemanHannah ne. Ban san inda take ba. Ba mu ganta ba tun da rana.

78. **KANDE:** (**COLDLY)** tana nan.

79. **DANJUMA:** **(RELIEF)** Alhamdulillah!

80. **KANDE:** Toh me ka ke so, Danjuma?

81**. DANJUMA:** **(TAKEN ABACK)** Ah ahn? Me kuma na k enema? Inaso inga matata in kuma kaita gida ta na lafiya?

82. **KANDE:** **(INCREDULOUS)** Mhnn. So Danjuma za ka zo gidan nan kamar bakayi komai ba, kamar babu abin day a faru.

83. **DANJUMA:** **(CONFUSED)** Gwaggo Kande, me kike tunani yafaru? Me ya faru? Me ya faru da Matata?

84. **KANDE:** Kwarai kamar yadda na sani, tana cikin wani mugun hali. Ina son ka gayamun abin da Hannah tayi maka da ka sata a cikin wannan hali. Me tayi maka da ka sata cikin wannan kazamin hah?

85. **DANJUMA:** **(STILL CONFUSED)** Gwaggo kande me kike nufi da wannan bayanin naki? Me nayi daba dai-dai ba? Me yasa Hannah ta shiga mugun hali?

86. **KANDE:** **(HISSES LOUDLY)** Kada ka dauke ni wawuya mana, Danjuma. Kana so kace mun baka san aibn day a faru ba?

87. **DANJUMA:** Gwaggo kande, don Allah mu fahimcijuna, gaya mun me yafaru.

88. **KANDE:** Toh Danjuma Ina son ka gayamu abin da kayi yau da rana.

89. **DANJUMA:** **(SUPPRISED)** Me nayi da ranan nan, banda barci? Na rantse bayan nag a taro a offis yau ranar gaba daya barcina tayi a gida.

90. **KANDE:** Kana gaya mun cewa kayi barci kai daya yau da rana a gida?

91. **DANJUMA:** Kwarai Gwaggo kande, Hannah bata gida. Ban ga ne abin da ki ke nufi ba.

92. **KANDE:** Hannah ta damu kwarai bayan taga Tina ta Fitowa daga Uwar dakinka yau da rana.

93. **DANJUMA:** **(SHOCKED)** Tana hauka ne? Ban taba kwara da Tina ba. Banma taba ganinta a uwar dakina ba.

94. **KANDE**: Amma yaya akayi Hannah ta ganku kuna kwance a daki daya da Tina har ma tina na da karfinhalin gaya mata cewa kai da ita kuna da ma'ammala tare.

95. **DANJUMA**: Kande, na maimaita, yau da rana barci na yi to yi kuma babu yadda za ayi in bar irin wannan sa'in sai haka nan.

96. **KANDE:** **(UPSET)** Na san Hannah babu yadda za'ayi ta kirkiro wannan labarin.

97. **DANJUMA:** Gwaggo kande na rantse bani da laifi a cikin wannan alamari. Don Allah bari in shiga cikin gidan in yi Magana da Hannah.

98. **KANDE:** **(SOUNDING CALM)** Toh, shigo ciki tan a cikin daki. Bari in ga ko zata yarda tayi Magana da kai.

99**. SFX:** **<u>DOOR OPENS WIDER AND CLOSES</u>**

100. **DANJUMA:** Tun lokacin da ban ganta ba, ina ta kiran layin ta, amma taki daukar waya ta.

101**. KANDE:** Kar ka damu, bari in shiga in yi mata Magana, na san baycan haka zata saurare ba.

102. **DANJUMA:** **(AGITATED)** Na gode Gwaggo Kande. Don Allah ki taimaka mun, saboda ban san abin da yake faruwaba.

103. **MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**